| | |
|---|---|
| **JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** | **8 Sha'aban, 1443** |
| **MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** | **11 Maris, 2022** |

## MATSAYIN SHAHIDAI A WURIN UBANGIJINSU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijin su ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani. Farin-ciki da murna sun lulluɓe fuskokin su sakamakon abin da Allah ya ba su na wasu abubuwa da aka keɓance su da su saboda falalar sa, suna kuma farin-ciki da murna da 'yan uwan sun da suka bari a raye a duniya suna tsaye akan hanyar imani da jahadi, da cewa lallai babu tsoron wani abin ƙi da zai same su, ba kuma sa baƙin-ciki saboda wani abu da suke so da ya kuɓuce masu. Fuskokin shahidai suna walƙiya saboda baiwar da Allah ya yi masu na ni'imar shahada, da ni'imar aljanna, da babban karramawar da aka yi masu, lallai shi Allah ba ya tozartar da ladan muminai)** [Ali Imran: 169- 171], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah mai girma da buwaya matsayi ne mai girma, babban hanya ce ta kusantar Allah Maɗaukakin Sarki, hasali ma shahada zaɓi da Allah Mai girma da

ɗaukaka yake yi wa gwarazan bayinsa da suka sadaukar da kawunansu wajen taimakon gaskiya da ba ta kariya, da kuma kwaɗayin bai wa ƙasa kariya, da samar da tsaro da aminci ga 'yan ƙasa, da kiyaye turbar ƙasar kanta, Allah Mai girma yana cewa: **(Saboda Allah ya bayyanar da waɗanda suka yi imani, ya kuma sanya su zama Shahidai)** [Ali Imran: 140].

Saboda haka ne Allah ya keɓance Shahidai da manyan matsayi da falala mai girma da karama ta ban mamaki, babban abin da yake nuni zuwa ga haka shi ne maganar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da yake cewa: **(Na rantse da wanda rai na yake hannunsa, na yi burin a kashe ni wajen ɗaukaka kalmar Allah, sannan a raya ne, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni).**

A cikin manyan matsayin da Shahidai suke da su akwai: kasancewar su rayayyu a wurin Ubangijinsu, rayuwa ce wadda ta zarce tunanin ɗan Adam, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Haƙuri ba ya taɓa kai wa zuwa ga komai sai alhairi da jin daɗin duniya da na lahira, kada ku ƙi zuwa yin jahadi domin ɗaukaka kalmar Allah, kada ku ji tsoron mutuwa a cikinsa, duk wanda ya rasu a wajen jahadi, to, a haƙiƙa ba matacce ne shi ba, rayayye ne shi rayuwa mai daraja, duk kuwa da cewa rayayyu ba su iya riskar haka)** [al- Baƙra: 154], An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: wata rana Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya haɗu da ni, sai ya ce mini: **(Ya Jabir, yaya na ganka ba ka da karsashi, duk ka karaya?)** Sai na ce: Ya Manzon Allah, baba na ne ya yi shahada, ya kuma bar 'ya'ya da bashi, sai ya ce: **(Ashe ba na yi maka albishir da abin da Allah ya tarbi babanka da shi ba?),**

Sai na ce: Na'am a faɗa mini ya Manzon Allah, sai ya ce: **(Allah bai taɓa yi wa wani magana ba sai ta bayan hijabi, amma babanka Allah ya yi magana da shi ba da hijabi ba, ya ce masa: (Ya bawana, mene kake buri, in ba ka? Sai ya ce: ya Ubangiji, ina da burin ka sake raya ni saboda a sake kashe ni a karo na biyu, sai Ubangiji Mai girma da buwaya ya ce: (Lallai hukunci na ya riga ya tabbata akan cewa bayi na da suka mutu ba za su koma duniya ba), sai Allah ya saukar da wannan ayar: (Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijin su ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani)** [Ali Imran: 169], kaman yanda Shahidai suke a raye a wurin Ubangijinsu mai girma da buwaya, haka ma suke a raye a cikin ruhi da zuciyar ƙasa, ba za a taɓa mancewa da gwarazantaka da bajintar da suka nuna ba komin daren daɗewa..

Haka ma rayukansu suna cikin ni'ima mai girma a wurin Ubangijinsu, suna shawaginsu a cikin aljanna yanda suke so, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lokacin da aka ci 'yan uwanku da yaƙi a yaƙin Uhudu, Allah ya sanya rayukansu a cikin wani koren tsuntsu, yana zuwa kogunan aljanna, yana cin kayan amfanin cikintae, sannan ya yi masu masauki a cikin wasu kyandura na zinare da aka rataye su a inuwar al' Arshi).**

Haka ma Shahidai sukan zama masu manyan lada, da cikakken haske a ranar alƙiyama, Allah mai girma yana cewa: **(Lallai Shahidai suna da lada mai girma gami da haske a wurin Ubangijinsu)** [al- Hadid: 19], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa Ummu Harisat Bn Suraƙat (Allah ya

ƙara yarda da shi) lokacin da ta yi tambaya game da makomar Harisat (Allah ya ƙara yarda da shi) bayan ya yi shahada a yaƙin Badar: **(Ummu Harisat, aljannatai ne masu yawa a aljanna, ɗanki ya sami Firdausi maɗaukakiya).**

Haka ma shahidai za su ceci iyalai da danginsu ƙa ranar alƙiyama, wannan sakamako ne daga Ubangijinsu mai girma da buwaya akan kyautata tarbiyyarsu da suka yi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam yana cewa: **(Shahidi zai ceci mutane saba'in cikin danginsa).**

Haka ma ladan ayyukansu ba sa yankewa, hasali ma haka za a cigaba da ba su cikakken lada, a kuma ninnika masu, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ana rufe shafin ayyukan kowane mamaci, banda wanda yam utu wajen ribaɗi saboda ɗaukaka kalmar Allah, lallai shi ayyukansa za su cigaba da haɓaka har zuwa ranar alƙiyama, za kuma a ba shi aminci ga barin fitinar kabari).**

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka wanda yake samun matsayin shahidi, shi ne wanda yake shahidi ne na gaskiya, wanda ya san gaskiya, ya kuma yi mata biyayya, ya ba ta kariya, ya sadaukar da kansu saboda ita, shi shahidi na gaskiya shi ne wanda yam utu wajen kare ƙasarsa da mutuncinsa, da kuma kiyaye tsaro da zaman lafiyar al'ummarsa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam yana cewa: **(Duk wanda aka kasha shi wajen bai wa dukiyarsa kariya shahidi ne, duk wanda aka kasha shi wajen**

**bai wa iyalansa kariya shahidi ne, ko wajen kare kansa, ko wajen kare addininsa shahidi ne).**

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa haƙiƙanin hanyar da za mu mutunta shahidanmu ita ce dukanmu mu zama sojoji na wannan ƙasar mai girma a duk fagen da muke, kowa daga cikinmu ya yi aiki tuƙuru wajen hidimta wa ƙasa, mu haɗa kai, mu goyi bayan jami'anmu na soja da na 'yan sanda da ma'aikatun gwamnati, sannan mu sanya fatan samun ladan shahidai a wurin Allah mai girma da buwaya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Duk wanda ya roƙi Allah y aba shi shahada da gaske, to kuwa Allah zai kais hi matsayin shahidai koda kuwa akan shinfiɗarsa ya rasu).**

**Ya Allah Ubangiji ka kare mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**